# Karfafawa don Kowace Rana

**Domin ta wurin hankuri
da ta'aziyar littattafai
mu zama da bege.
Romawa 15 : 4.**

***SGM International***
*3 Eccleston Street*
*London SW1W 9LZ*

*Printed in Great Britain*

## Abin lura ga Mai-karatu

Wannan ɗan littafi ya zama sanadin kawowan ta'aziya da bege mai-kyau ga mutane masu yawa, cikin aikowa da ita kamar yadda ta ke, ana tuna ma mai-karatu waɗannan alkawalan Allah domin waɗanda suka bada gaskiya ne ga Maganar Allah suka karɓi Ubangiji Yesu Kristi kaɗai Macecinsu daga zunubi da fidda zuciya.

Ana roƙonka da naciya ka sami Littafi Mai-Tsarki da kanka, domin shi ne da bayanin Gaskiya na Allahntaka.

Za ka iya samu wasu sashen Littafi Mai-Tsarki idan ka rubuta ma:—

**Scripture Gift Mission**

Eccleston Street,
London, SW1W 9LZ.

Maganar Allah mai-rai ce,
mai-aikatawa, ta fi kowane
takobi mai-kaifi biyu ci.
Ibraniyawa 4 : 12.

Maganata . . . ba za ta koma
wurina wofi ba, amma za
ta cika
abin da na nufa, za ta yi
albarka kuma a cikin sakona.
Ishaya 55 : 11.

Buɗen zantattukanka
yana ba da haske.
Zabura 119 : 130.

# Maganganun Ta'aziyya

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce:
Kada zuciyarku
ta ɓaci
kuna bada gaskiya ga Allah,
ku bada gaskiya gareni kuma.
Salama ina bar maku,
salamata
ni ke ba ku
ba kamar yadda duniya ke
bayaswa
ni, ni ke ba ku ba.
Kada zuciyarku
ta ɓaci
kada ta ji tsoro kuma.
Yohanna 14 : 1, 27.

Ku zo gareni, dukanku da ku
ke wahala,
masu-nauyin kaya kuma, ni
kwa im ba ku hutawa.
Matta 11 : 28.

## Rana ta fari

Ya Ubangiji, ni mutum mai-zunubi ne.
Luka 5 : 8.

—

Allah yana shaidar
ƙauna-tasa gare mu, da ya ke,
tun muna masu-zunubi tukuna,
Almasihu ya mutu
sabili da mu.
Romawa 5 : 8.

Allah ya ce,
Na yi ƙaunarka da
madawamiyar ƙauna;
domin wannan na
jawo ka da rahama.
Irimiya 31 : 3.

Allah ya ba mu
rai na har abada,
wannan rai kuma cikin
Ɗansa ya ke.
1 Yohanna 5 : 11.

# Rana ta biyu

**Ka tokare ni, ni kwa zan zauna lafiya.**
Zabura 119 : 117.

---

Allah mafakammu ne da
ƙarfinmu,
taimako ne na kurkusa
cikin wahala.
Zabura 46 : 1.

Allah madawami shi ne
mazamninka,
ƙalƙashinka kuma
madawaman hannuwa su ke.
Kubawar Shari'a 33 : 27.

Allah ya ce:
Ni ƙarfafa ka;
ni taimake ka, i, ni
riƙe ka da
hannun dama na
adilcina.
Ishaya 41 : 10.

# Rana ta uku

Kada ka nisa da ni; gama wahala
tana kusa.
Zabura 22 : 11.

---

Allah ya ce:
Ka kira bisa gare ni kuma cikin
ranar masifa;
zan cece ka, za ka
girmama ni kuma.
Zabura 50 : 15.

Ka zuba nawayarka bisa
Ubangiji,
shi kuma za ya agaje ka.
Zabura 55 : 22.

A cikin ranar wahala
zai ɓoye ni cikin
bukkarsa;
a cikin maɓoyar tent nasa
zai suturce ni;
zai ɗaukaka ni bisa pa.
Zabura 27 : 5.

# Rana ta fudu

Ubana, na yi zunubi a gaban sama,
a gabanka kuma.
Luka 15 : 21.

---

Ubangiji cike da tausayi ya ke
mai-nasiha,
mai-jinkiri fushi, mai-yalwar
jinƙai kuma.
Zabura 103 : 8.

Allah ya ce:
Zan warkadda ɓaraicinsu,
zan ƙaunace su a yalwace;
gama fushina ya kawu.
Hosea 14 : 4.

Nagari ne kai,
ya Ubangiji,
mai-hamzarin gafartawa kuwa,
mai-yawan jinƙai ga
dukan waɗanda su ke kira gare
ka.
Zabura 86 : 5.

## Rana ta biyar

Ni matalauci ne, mai-mayata kuma,
ya Allah.
Zabura 70 : 5.

---

Allahna zai biya
kowace bukatarku
gwalgwadon wadatassa cikin
daraja cikin Almasihu Yesu.
Filibbiyawa 4 : 19.

Wanda ba ya keɓe
Ɗa nasa ba,
amma ya bashe shi domin
mu duka, ƙaƙa zai rasa
ba mu abu duka kuma
tare da shi a yalwace?
Romawa 8 : 32.

Ka damƙa ma Ubangiji
tafarkinka;
ka dogara gare shi;
shi kuma zai tabbatadda shi.
Zabura 37 : 5.

## Rana ta shidda

Kada ka yarfadda ni, ya Allah,
kada ka yashe ni.
Zabura 27 : 9.

---

Ubangiji shi ke
cike da tausayi,
mai-jinƙai kuma.
Yakub 5 : 11.

Lallai zai yi
maka rahama yayinda ya
ji muryar kukanka;
sa'anda ya ji kwa,
zai amsa maka.
Ishaya 30 : 19.

Ubangiji
yana kusa
da dukan waɗanda
su ke kira
bisa gareshi.
Zabura 145 : 18.

**Rana ta bakwai**

**Ka sa in san tafarkin da zan bi.**
Zabura 143 : 8.

---

Ubangiji
zai ja maka hanya
tuttur.
Ishaya 58 : 11.

Ubangiji ne
zai tafi gabanka;
shi zamna
tare da kai,
ba zai bar ka ba,
ba kwa zai yashe
ka ba.
Kubawar Shari'a 31 : 8.

Wannan Allah Allahnmu ne
har abada abadin,
zai zama ja gabanmu
har zuwa mutuwa.
Zabura 48 : 14.

## Rana ta takwas

—

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Sai in sake dawowa
in karɓe ku wurin kaina;
domin wurin da ni ke,
ku zauna kuma.
Yohanna 14 : 3.

Kadan an bayana shi,
mu za mu zama kamansa
gama za mu gan shi
kamar yadda shi ke.
1 Yohanna 3 : 2.

Sa'anda Almasihu
wanda shi ne ranmu, ya bayana,
sa'annan ku kuma
tare da shi za ku bayana
cikin daraja.
Kolossiyawa 3 : 4.

—

Ka zo, ya Ubangiji Yesu.
Ru'ya ta Yohanna 22 : 20.

## Rana ta tara

Ya Ubangiji . . . ka zama pa
mai-ƙarfi gareni.
Zabura 31 : 1, 2.

—

Ku dogara ga
Ubangiji
har abada:
gama cikin
Ubangiji Yahweh akwai
madawamin dutse.
Ishaya 26 : 4.

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce:
Alherina ya ishe ka:
gama cikin kumamanci
ikona ya ke cika.
2 Korinthiyawa 12 : 9.

Yesu Almasihu
ɗaya ne da jiya,
da yau, i,
har abada kuma.
Ibraniyawa 13 : 8.

## Rana ta goma

**Ya Ubangiji, ina bada gaskiya, ka taimake ni da rashin bangaskiya.**
Markus 9 : 24.

---

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Kada zuciyarku ta ɓaci:
kuna bada gaskiya ga Allah,
ku bada gaskiya gare ni kuma.
Yohanna 14 : 1.

Gama na kawas da shakka,
ba mutuwa, ba rai,
ba mala'iku, ba sarautai,
ba al'amuran yanzu,
ba al'amura na zuwa,
ba ikoki, ba tsawo, ba zurfi,
ba kwa wani halittacen abu,
da zai iya raba mu
da ƙaunar Allah,
wadda ke cikin Almasihu Yesu
Ubangijinmu.
Romawa 8 : 38, 39.

## Rana ta goma sha ɗaya

Kada ka tuna da zunubaina
na ƙuruciya.
Zabura 25 : 7.

---

Allah ya ce,
Kada ka ji tsoro,
gama na panshe ka,
ina yi kiranka
da sunanka,
kai nawa ne.
Ishaya 43 : 1.

Ni, i, ni ne
na shafe
laifofinka sabili
da ƙauna:
ba ni kuwa ƙara tuna da
zunubanka ba.
Ishaya 43 : 25.

Kada ka ji tsoro
gama ina tare da kai.
Ishaya 41 : 10.

## Rana ta goma sha biyu

Karfina yana kāsawa saboda
muguntata.
Zabura 31 : 10.

---

Ubangiji yana
kusa da
masu-karyayyar zuciya,
yana ceton irin
waɗanda su ke da
ruhu mai-tuba.
Zabura 34 : 18.

Ka ƙarfafa
ka yi ƙarfin zuciya kuma;
gama Ubangiji Allahnka
yana tare da kai
dukan inda ka nufa.
Joshua 1 : 9.

Ubangiji
zai bada ƙarfi
ga mutanensa.
Zabura 29 : 11

## Rana ta goma sha uku

Ya Ubangiji . . . ka ji muryar
addu'oina.
Zabura 28 : 1, 2.

---

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Hakika, hakika, ina ce maku,
idan kun roƙi kome
ga Uba
zai ba ku a cikin sunana.
Yohanna 16 : 23.

Dukan abu, kuma,
iyakar abin da za ku
roƙa cikin addu'a, kuna bada
gaskiya za ku karɓa.
Matta 21 : 22.

Kowane mai-roƙo
yana karɓa;
mai-nema kuma yana samu;
wanda ya ke ƙwanƙwasawa
kuma za a buɗe masa.
Luka 11 : 10.

**Rana ta goma sha hudu**

Tashi, ya Ubangiji; ka cece ni.
Zabura 3 : 7.

—

Allah ya aiko 'Dan
cikin duniya
ba domin ya yi ma
duniya shari'a ba;
amma domin duniya
ta tsira ta wurinsa.
Yohanna 3 : 17.

Dukan wanda
zai kira bisa
sunan Ubangiji
zai tsira.
Romawa 10 : 13.

A wurin Ubangiji
akwai jinƙai,
a wurinsa kuma
da pansa yalwataciya.
Zabura 130 : 7.

# Rana ta goma sha biyar

Ubanmu . . . ka cece mu daga Mugun.
Matta 6 : 9, 13.

---

Allah
mai-aminci ne
da ba zai bari
a yi maku jaraba
wadda ta fi ƙarfinku ba;
amma tare da jaraba
zai yi maku hanyar tsira,
da za ku iya
jimrewa.
1 Korinthiyawa 10 : 13.

Ubangiji
ya san yadda
za ya ceci
masu-ibada
daga cikin
jaraba.
2 Bitrus 2 : 9.

# Rana ta goma sha shidda

**Ya Allah . . . ka tsarkake ni daga zunubina.**
**Zabura 51 : 1, 2.**

---

Mu zo, yanzu, mu yi bincike
tare, in ji Ubangiji:
ko da
zunubanku sun yi kamar
mulufi
za su yi fari kamar snow:
ko da suna ja wur kamar
garura za su
zama kamar abduga.
Ishaya 1 : 18.

An gafarta maku zunubanku
sabili da sunansa.
1 Yohanna 2 : 12.

Sabili da laifofinmu ne
aka yi masa rauni,
aka ƙuje shi
domin kurakuranmu.
Ishaya 53 : 5.

**Rana ta goma sha bakwai**

Ubangiji, na bada gaskiya kai ne
Almasihu 'Dan Allah.
Yohanna 11 : 27.

---

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Kamar yadda Musa ya ta da
maciji bisa cikin jeji,
hakanan kuma dole
za a ta da 'Dan mutum bisa;
domin dukan wanda
ya ke bada gaskiya gare shi
ya sami rai na har abada.
Gama Allah ya yi
ƙaunar duniya
har ya ba da
'Dansa, haifaffe shi kaɗai,
domin dukan wanda
ya ke bada gaskiya gare shi
kada ya lalace
amma ya sami rai na
har abada.
Yohanna 3 : 14-16.

## Rana ta goma sha takwas

Ya Allah . . . kada ka yashe ni
daga gabanka.
Zabura 51 : 10, 11.

---

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce:
Ku zo gareni,
dukanku da ku ke wahala
masu-nauyin kaya kuma,
ni kwa im ba ku hutawa.
Matta 11 : 28.

Wanda ya zo gareni kuwa
ba ni fitarda shi
ba ko kaɗan.
Yohanna 6 : 37.

Ni ne gurasa ta rai:
wanda ya zo gareni
ba zai ji yunwa ba
wanda ya bada gaskiya gareni
kuma
ba zai ji ƙishi ba daɗai.
Yohanna 6 : 35.

# Rana ta goma sha tara

Ya Allah, ka shafe laifofina.
Zabura 51 : 1.

---

Allah ya ce: Na shashafe laifofinka
kamar hadari baƙi ƙirin,
kamar girgije kuma zunubanka:
ka komo
wurina; gama na panshe ka.
Ishaya 44 : 22.

Ba ya aika mamu
gwalgwadon zunubanmu ba;
ba ya saka mamu
gwalgwadon laifofinmu ba.
Gama kamar yadda sama
ta yi nisa birbishin duniya,
hakanan kuma jinƙansa yana
da girma
zuwa ga masu-tsoronsa.
Kamar nisan gabas da yamma,
hakanan ya kawas da saɓe
saɓenmu ya nisantadda su.
Zabura 103 : 10-12.

## Rana ta ashirin

Ni tashi, in tafi wurin ubana.
Luka 15 : 18.

---

Domin Almasihu kuma
ya sha azaba sabili da
zunubai sau ɗaya
mai-adilci sabili da
marasa adilci,
domin shi kawo mu ga
Allah.
1 Bitrus 3 : 18.

Amma yanzu cikin Almasihu
Yesu ku da ku ke
manisanta a dā, cikin jinin
Almasihu
an maishe ku kusa.
Afisawa 2 : 13.

Babu kayaswa fa yanzu
ga waɗanda
ke cikin Almasihu Yesu.
Romawa 8 : 1.

## Rana ta ashirin da ɗaya

Ya Allah . . . ka ɓoye ni ƙalƙashin
inuwar fukafukanka.
Zabura 17 : 6, 8.

---

Kuna zuba dukan
alhininku
a bisansa,
domin yana
kula da ku.
1 Bitrus 5 : 7.

Shi da kansa ya ce,
Daɗai ba ni tauye maka ba,
daɗai kwa ba ni
yashe ka ba.
Ibraniyawa 13 : 5.

Kaunatacen Ubangiji
za ya zamna lafiya
kusa da shi;
duk yini
yana rufe da shi.
Kubawar Shari'a 33 : 12.

## Rana ta ashirin da biyu

Ya Allah, ka kiyaye ni: gama gareka
ni ke dogara.
Zabura 16 : 1.

---

Ubangiji ne mai-tsaronka
Ubangiji shi ne inuwarka ga
hannun damanka.
Ubangiji za ka
tsare ka daga
dukan mugunta:
Za ya kiyaye ranka.
Ubangiji za ya tsare
fitarka da shigarka
daga yanzu
har abada kuma.
Zabura 121 : 5, 7, 8.

Za ka riƙe shi
cikin cikakkiyar salama
shi wanda hankalinsa yana kafe
bisa gareka: saboda
yana dogara gareka.
Ishaya 26 : 3.

## Rana ta ashirin da uku

Ya Allah . . . Ka wanke ni, zan kwa
fi snow fari.
Zabura 51 : 1, 7.

---

Jinin
Yesu 'Dansa
yana tsarkake mu kuma daga
zunubi duka.
1 Yohanna 1 : 7.

Wanda muna da
pansarmu a cikinsa
ta wurin jininsa,
gafarar laifofinmu.
Afisawa 1 : 7.

Kuma babu
ceto ga waninsa
gama babu wani suna
ƙalƙashin sama da aka bayas
wurin mutane,
inda ya isa mu tsira.
Ayukan Manzanni 4 : 12.

## Rana ta ashirin da fudu

Daga cikina ka halitta zuciya
mai-tsabta, ya Allah.
Zabura 51 : 10.

---

Duba,
ga Ɗan rāgo na Allah
wanda yana ɗauke da
zunubin duniya.
Yohanna 1 : 29.

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Hakika, hakika,
ina ce maku,
wanda yana bada gaskiya
yana da rai na har abada.
Yohanna 6 : 47.

Ga shi,
yanzu ne lokaci
na alheri; ga shi,
yanzu ne ranar ceto.
2 Korinthiyawa 6 : 2.

## Rana ta ashirin da biyar

Ubangiji, ka taimake ni.
Matta 15 : 25.

—

Allah ya ce,
Ni dai, ni ne
mai-yi maku
ta'aziya.
Ishaya 51 : 12.

Kamar
wanda uwatasa
ta ke yi masa ta'aziya,
hakanan zan
ta'azantadda
ku.
Ishaya 66 : 13.

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Ba ni barin ku
marayu ba
Ni zo wurinku.
Yohanna 14 : 18.

## Rana ta ashirin da shidda

**Ya Allah . . . ka bada ƙarfinka ga bawanka.**
**Zabura 86 : 14, 16.**

---

Gama ka zama
kagara ga matalauta
kagara
ga mai-mayata
a cikin ƙuncinsa,
mafaka
daga hadari
inuwa daga zafi.
Ishaya 25 : 4.

Ubangiji kuma za ya zama
kagara mai-tsawo domin
waɗanda a ke zalumtassu,
kagara mai-tsawo cikin
wokatan wahala.
Zabura 9 : 9.

Ba ya fasa ba.
Zephaniah 3 : 5.

## Rana ta ashirin da bakwai

**Ka kasa kunne ga addu'ata, ya Allah.**
Zabura 55 : 1.

---

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce:
Ku roƙa
za a ba ku;
ku nema
za ku samu;
ku ƙwanƙwasa
za a buɗe maku.
Matta 7 : 7.

Dukan iyakar abin da
ku ke addu'a kuna roƙo kuma,
ku bada gaskiya kun rigaya kun karɓa
za ku samu fa.
Markus 11 : 24.

Idan kun roƙe ni komi
a cikin sunana,
Ni yi wannan.
Yohanna 14 : 14.

## Rana ta ashirin da takwas

Ya Ubangiji . . . Ka ceci ni cikin
rahamarka.
Zabura 31 : 14, 16.

---

Ɗan Mutum
ya zo
garin neman abin da
ya ɓace ya
cece shi kuma.
Luka 19 : 10.

Da kansa fa ya
ɗauki zunubanmu ya
kai su cikin jiki nasa
bisa itacen.
1 Bitrus 2 : 24.

Kowane
mai-bada gaskiya
gareshi
za ya sami gafarar
zunubai.
Ayukan Manzanni 10 : 43.

**Rana ta ashirin da tara**

Ya Allah, ka yi mani jinƙai,
ni mai-zunubin.
Luka 18 : 13.

---

Almasihu Yesu ya zo cikin
duniya
domin ceton masu-zunubi.
1 Timothawus 1 : 15.

Hannun Ubangiji ba ya yi
gajarta ba, har da ba ya iya
ceto ba; kunnensa kwa ba ya
yi nauyi ba, har
da ba za ya iya ji ba.
Ishaya 59 : 1.

Yana da iko ya yiwo ceto
ba iyaka
domin waɗanda
ke kusantawa ga Allah ta wurinsa.
da shi ke kullum a raye ya ke
domin yin roƙo sabili da su.
Ibraniyawa 7 : 25.

## Rana ta talatin

Malam, mi zan yi domin in gāji
rai na har abada?
Luka 10 : 25.

---

Ubangiji Yesu Almasihu ya ce,
Ni ne makiyayi mai-kyau
makiyayi mai-kyau ya kan bada
ransa domin tumaki.
Tumakina
suna jin muryata
na kwa san su, suna
biyona kuma: ina ba su
rai na har abada;
Ba kwa za su lalace ba dađai
ba wanda za ya ƙwace su
daga cikin
hannuna kuma.
Yohanna 10 : 11, 27, 28.

Domin ni ina da rai, ku kuma
za ku rayu.
Yohanna 14 : 19.

## Rana ta talatin da ɗaya

Yesu, ka tuna da ni lokacinda ka
shiga mulkinka.
Luka 23 : 42.

—

Allah,
domin mawadaci ne cikin jinƙai
saboda ƙaunassa mai-yawa
wadda
ya ƙaunace mu da ita,
ko lokacinda mu ke
matattu ta wurin laifofinmu,
ya rayadda mu tare da Almasihu
(ta wurin alheri an cece ku;)
ya tashe mu
tare da shi, ya zamshe mu
tare da shi, cikin sammai
cikin Almasihu Yesu.
Afisawa 2 : 4-6.

Ga shi Allah ne cetona
zan dogara,
ba kwa zan yi tsoro ba.
Ishaya 12 : 2.

# Zabura 1

Mai-albarka ne mutum wanda ba ya bi ta shawarar miyagu ba, ba ya tsaya a cikin tafarkin masu-zunubi ba, ba ya zamna a cikin mazamnin masu-ba'a ba.

Amma marmarinsa cikin shari'a ta Ubangiji ya ke; kuma a cikin shari'assa ya kan rika tunani dare da rana.

Za ya zama kamar itacen da aka dasa a magudanan ruwaye, wanda yana bada y'ay'ansa a cikin kwanakinsa; ganyensa ba ya yi yaushi ba; kuma cikin iyakar abin da ya ke yi za shi yi albarka.

Ba hakanan miyagu su ke ba; amma suna kama da ƙaiƙai wanda iska ya ke shiƙassa.

Domin haka miyagu ba za su tsaya a cikin ranar shari'a ba, ko masuzunubi a cikin jama'ar masu-adilci.

Gama Ubangiji ya san hanyar masu-adilci: amma hanyar miyagu za ta lalace.

## Zabura 23

Ubangiji makiyayina ne; ba zan rasa komi ba.

Yana sanya ni in kwanta a cikin makiyaya mai-ɗanya: yana bishe ni a gefen ruwaye na hutawa.

Yana wartsakadda raina; yana bishe ni a cikin hanyoyin adilci sabili da sunansa.

Hakika, ko tafiya ni ke yi ta tsakiyar kwari na inuwar mutuwa, ba zan ji tsoron kowace masifa ba: gama kana tare da ni; sandarka da kerenka suna yi mani ta'aziya.

Ka kan shirya table a gabana a idanun maƙiyana: ka shafe kaina da mai; ƙoƙona ya cika har yana zuba.

Nagarta da jinƙai kaɗai za su bi ni dukan kwanaķin raina: zan zamna kuma a cikin gidan Ubangiji har abada.

## Zabura 27

Ubangiji ne haskena da cetona kuma; tsoron wa zan ji? Ubangiji shi ne ƙarfin raina; zan ji tsoron wanene?

Lokacin da masu-mugunta suka afko mani domin su cinye namana, su abokan gabana da maƙiyana, tuntuɓe suka yi suka fāɗi.

Ko rundunar yaƙi za ta kafa mani sansani, zuciyata ba za ta ji tsoro ba: ko yaƙi za shi taso mani, duk da wannan a natse ni ke.

Abu guda ɗaya na yi roƙo ga Ubangiji, shi zan nema; in zamna cikin gidan Ubangiji dukan kwanakin raina, domin in dubi jamalin Ubangiji, in yi tunani cikin haikalinsa.

Gama a cikin ranar wahala za shi ɓoye ni cikin bukkarsa: a cikin maɓoyar tent nasa za ya suturce ni; za ya ɗaukaka ni bisa pa.

Yanzu kuma za a ɗaukaka kaina bisa maƙiyana da su ke kewaye da ni; ni ma zan bada hadayu na farinciki a cikin tent nasa: zan raira, i, zan raira yabo ga Ubangiji.

Da ba domin na gaskanta zan ga alherin Ubangiji a cikin ƙasa ta masu-rai, da na suma.

Ka yi sauraro ga Ubangiji: ka ƙarfafa, ka bar zuciyarka ta ɗauki ƙarfin rai; i, ka yi sauraro ga Ubangiji.

Nassi 1-6, 13, 14.

## Zabura 34

Zan albarkaci Ubangiji a kowane loto: yabonsa kwa za ya zamna a bakina tuttur.

Raina za shi yi fahariya a cikin Ubangiji: mai-tawali'u za ya ji, ya yi murna kuma.

Ku girmama Ubangiji tare da ni, bari kuma mu ɗaukaka sunansa tare.

Na ɓidi Ubangiji, ya amsa mani ya kuma tsamadda ni daga dukan yawan tsorona.

Suka duba gareshi, suka haskaka; fuskokinsu kuma ba za su kumyata ba daɗai.

Wannan talaka ya yi kuka, Ubangiji kuma ya ji shi, ya cece shi daga dukan wahalansa.

Malaikan Ubangiji yana kafa sansani a kewaye da masu-tsoronsa, yana tseradda su kuma.

Ku ɗanɗana, ku duba Ubangiji nagari ne: mai-albarka ne mutum wanda ya ke dogara gareshi.

Ku ji tsoron Ubangiji, ku tsarkakansa: gama babu rashi ga masutsoronsa.

Yayan zaki su kan rasa, su kan ji yunwa: amma waɗanda su ke biɗan Ubangiji ba za su rasa kowane abu mai-kyau ba.

Ku zo, ku yara, ku kasa kunne gareni: ni koya maku tsoron Ubangiji.

Wane mutum ne wanda ya ke son rai, shina begen yawan kwanaki kuma, da za shi ga alheri?

Ka kiyayadda harshenka ga barin mugunta, leɓunanka kuma ga barin maganar algus.

Ka rabu da mugunta, ka yi nagarta; ka biɗi salama, ka bi ta kuma.

Idanun Ubangiji suna fuskanta wajen masu-adilci; kunnuwansa kuma a buɗe su ke ga jin ƙarassu.

Fuskar Ubangiji tana gāba da masu-aikin mugunta, domin ya shafe tunawa da su daga duniya.

Masu-adilci suka yi kuka, Ubangiji ya ji, ya tsamadda su daga dukan wahalansu.

Ubangiji yana kusa da masu-karyayyar zuciya, yana ceton irin waɗanda su ke da ruhu mai-tuba.

Masifu na mai-adilci dayawa su ke: amma Ubangiji ya kan tsamadda shi daga cikinsu duka.

Yana kiyaye dukan ƙasusuwansa, ko ɗaya cikinsu ba ya karye ba.

Mugunta za ta kashe miyagu: kuma waɗanda suna ƙin masu-adilci za a kāda su.

Ubangiji yana pansar ran bayinsa; a cikin masu-dogara gareshi ba za a kāda ko ɗaya ba.

## Zabura 91

Mai-zama cikin suturar Maɗaukaki za ya dawama a ƙalƙashin inuwar mai-iko duka.

Zan ce da Ubangiji, Shi ne mafakata da marayata kuma; Allahna, a gareshi ni ke dogara.

Gama za ya fishe ka daga tarkon mai-farauta, daga aloba mai-kawo mutuwa kuma.

Za shi rufe ka da jawarkinsa, a ƙalƙashin fukafukansa za ka sami kariya: gaskiyarsa garkuwa ce da kutufani.

Ba za ka ji tsoron razanar dare ba; ko kwa kibiya wadda ke tashi da rana;

Ko aloban da ke yawo a cikin dufu; ko hallaka wadda ke lalataswa da tsaƙar rana;

Mutum dubu za su faɗi daura da kai, zambar goma kuma a hannunka na dama; amma ba za ta kusance ka ba.

Da idanunka kadai za ka duba, ka ga sakamakon miyagun mutane.

Gama kai ne mafakata, ya Ubangiji! ka maida Madaukaki wurin zamanka;

Babu mugunta da za ta same ka, babu wata aloba da za ta kusanci tent naka.

Gama za ya ba malaikunsa tsaronka su kiyaye ka cikin tafarkunka duka.

Za su talafa ka a bisa hannuwansu, domin kada ka buga ƙarfarka a dutse.

Za ka taka zaki da tandara; ɗan zaki da mesa kuma za ka tattaka ƙalƙashin sawunka.

Tun da ya ƙallafa ƙaunassa a gareni, domin wannan zan tsamadda shi: Zan ɗaukaka shi, domin ya san sunana.

Za shi kira bisa gareni, ni kuma zan amsa masa; a cikin ƙunci ina tare da shi: zan tsamadda shi, zan kuma girmama shi.

Zan ƙosadda shi da tsawon rai, zan bayana masa cetona kuma.

## Zabura 121

Zan tada idanuna ga duwatsun: daga ina taimakona za ya fito?

Daga wurin Ubangiji taimakona ya ke fitowa, shi wanda ya yi sama da duniya.

Ba za ya bari a kwashe ƙafarka ba: shi wanda ya ke tsaronka ba za ya yi gyangaɗi ba.

Duba, shi wanda ya ke tsaron Israila ba za ya yi gyangaɗi ko barci ba.

Ubangiji ne mai-tsaronka: Ubangiji shi ne inuwarka ga hannun damanka.

Rana ba za ta buge ka cikin yini ba, ko wata da dare.

Ubangiji za ya tsare ka daga dukan mugunta: za ya kiyaye ranka.

Ubangiji za ya tsare fitarka da shigarka, daga yanzu har abada kuma

## Zabura 145

Zan ɗaukaka ka, ya Allahna, ya Sarki; zan albarkaci sunanka kuma har abada abadin.

Kowace rana zan albarkace ka; zan yabi sunanka kuma har abada abadin.

Mai-girma ne Ubangiji, ya kwa isa yabo ƙwarai; girmansa kuma ya fi gaban bincike.

Tsara za ta yaba ma tsara ayukanka, su bayana ayukanka masu-iko.

Zan yi bimbini da mashahuriyar ɗaukaka ta darajarka, da dukan ayukanka masu-ban mamaki.

Mutane kuma za su ambata ikon ayukanka masu-ban razana; Ni ma in bayana girmanka.

Za su furta zancen alherinka mai-girma, su raira adilcinka.

Nassi 1-7.